*Wannan fassarar Kungiyoyin Social Development Direct da Translators*

*without Borders suka yi ta da manufar sanarwa kawai. BOND ba za su iya tabbatar da daidai din sa ba. Sigar*

*kawai da aka amince da ita a hukumance an rubuta ta a turance wanda za'a iya samu a shafin yanar gizo na*

*BOND [*[Safeguarding policy templates | Bond]*].'*

# Kiyayewa ta Bond
# Dokokin Aiki

## Gabatarwa

Don cika burin manufarsu da dabi'unsu, [NGO] sun jajirce wajen tabbatar da mafi girman halayyar da'a a tsakanin dukkan ma'aikatansu da abokan aiki. Don taimakawa ƙara fahimta, wannan Dokokin Aiki yayi cikakken bayanin abubuwan da ake tsammani daga ma'aikatan [NGO] a ɓangarori muhimmai.

## Abubuwan da ya ƙunsa da manufa

Wadannan Dokokin Aiki sun shafi dukkan ma'aikatan da aka dauka kwangila, na ƙasa da ƙasa da kuma 'yan ƙasar wadanda [NGO] suka ɗauka aiki. Dokokin Aiki da aka sauya sun shafi masu aikin sa kai, abokan aiki, 'yan kwangila da masu kawo kaya.

Dalilin wannan Dokokin Aiki shi ne don bayyana halayen da ake tsammani daga ma'aikatan [NGO] yayin da suke da kwangila da ƙungiyar, kuma ya zama daga cikin dukkan kwangilar ɗaukan aiki. Wannan Ka'ida tana aiki a dukkan lokuta. Sabawa Ka'idodin Aikin ya zama hujjar daukar matakan ladabtarwa, har ya iya kai wa ga kuma har da kora daga aiki.

Yayin gane cewa dokoki na gida da al'adu sun bambanta sosai daga wata ƙasa zuwa wata, [NGO] wata Kungiya ce Mai Zaman Kanta ta Kasa da ƙasa, kuma don haka an gina Ka'idojin Aikin daga dokokin UN da sauran ka'idoji na ƙasa da ƙasa. Ma'aikatan [NGO] ana tsammanin za su bi dokar gida duk inda suke aiki, sai dai idan Ka'idojin Aikin ya fi tsanani, wanda in haka ne ka'idojin ne za'a bi.

## Manufa da dabi'u

[Shigar da Bayanin Manufar NGO ko Dabi'un Kungiya a nan]

## Tsayayyun Ka'idojin Aiki

*Godiya ga CHS Alliance*

A matsayin ma'aikacin [NGO] Zan:

**Kare mutuncin da sunan [NGO] ta tabbatar da cewa halina na kwarewar aiki da na karan kaina zai daidaitu da tsayayyun dabi'un [NGO]**

- Zan kula da dukkan mutane da adalci tare da daraja su da mutuntawa
- Yayin aiki a wani yanayi na kasa da kasa ko tafiya zuwa wata ƙasa a madadin [NGO], Zan lura da dukkan dokoki na gida kuma in yi la'akari da al'adun garin
- Zan nemi tabbatar da cewa halina ba zai jawowa [NGO] jayayya ba kuma ba zai yi tasiri akan ko fi ƙarfina wajen yin aikin da aka ɗauke ni ba
- Ba zan yi aiki a buge ba, ko amfani da barasa ba, ko mallakar miyagun ƙwayoyi a wurin aikin [NGO] ko masaukinsu ba

**Ba zan shiga halin zage-zage ko ci da gumi ba**

- Ba zan aikata jimai da yara ba (mutanen da suke ƙasa da shekaru 18). Kuskure a shekarun yaro/yarinya ba hujjar kare kai ba ne
- Ba zan yi musaya da kuɗi, aiki, kaya ko hidimomi don jima'i ba har da alfarmar jima'i ko sauran nau'in halayyar wulakanci, kaskantarwa ko ci da gumi ba, an haramta. Wannan ya hada da kowane musayar taimako da ya kamata ma su cin gajiyar su samu
- Ba zan shiga dangantakar jima'i tare da masu cin gajiyar taimako ba, tunda sun danganci kasancewar rashin daidaiton iko
- Ba zan shiga kowane ayyukan ci da gumi don kasuwanci tare da yara ko manyan da ka iya zama cikin haɗari har da bautar da yaro/yarinya ko fataucin mutane ba
- Ba zan farmaki yaro/yarinya ba a zahiri ko babba da ka iya zama cikin haɗari
- Bazan ci zarafin yaro/yarinya ko babba da ka iya zama cikin haɗari ta shauki ko tunani ba

**Tabbatar da tsaro, lafiya da walwalar dukkan ma'aikatan [NGO] da mai alhakin gudanarwa (masu aikin sa kai, abokan haɗin gwiwa, masu kawo kaya da 'yan kwangila)**

- Zan bi dukkan buƙatun shari'ah da lafiya da tsaron ƙungiyar da aka kafa a inda nake aiki
- Zan bi kowane jagororin tsaro na gida kuma in sanar da hukumar gudanarwa da wuri akan kowane canjin da ya zama dole zuwa waɗancan jagororin
- Zan nuna hali yadda zan guji kowane haɗari da bai kamata ba ga tsaro, lafiya da walwalar kaina da ta wasu, har da kungiyoyin da ake haɗin gwiwa da su da al'umman da muke aiki da su

**Zama mai ɗaukan alhakin amfani da bayanai, kayayyaki da albarkatun da nake samun damarsu don dalilin aikina da [NGO]**

- Zan tabbatar cewa Ina amfani da kayayyaki da albarkatun [NGO] da aka ban amanarsu ta hanyar da ya dace kuma zan ɗauki alhakin dukkan kuɗi da dukiya
- Ba zan yi amfani da kayayyakin IT, manhajar na'ura mai ƙwaƙwalwa ko e-mail da dandalin kafofin sada zumunta na [NGO] don yin ayyukan da ba bisa doka ba a karkashin doka ta gida ko ta ƙasa da ƙasa wanda ke jaddada halin da zai zama laifi. Wannan ya hada da kowane kayan da zai tsoratar, tursasa kowane rukunin mutane bisa ga siffofin da ake karewa, ko karfafawa ta'addanci
- Ba zan yi amfani da kayan IT na [NGO] don kallo, sauke, kirkiro, rarraba ko ajiye kowane kayayyaki da ba su dace ba ko kayan rashin mutunci har da amma bai tsaya ga batsa ko nunin cin zarafin yaro/yarinya ba

**Aiwatar da ayyukana kuma tafiyar da rayuwata yadda zan guji son zuciya**

- Zan bayyana kowane ra'ayin kuɗi, na kaina ko iyali (ko dangantaka mafi kusa) a al'amuran aikin ofis wanda zai iya tasiri akan aikin [NGO]
- Ba zan shiga ba da da fa'idodi, kwangilar kawo kaya ko hidimomi, ɗaukan aiki ko ƙarin matsayi a cikin [NGO], ga kowane mutumin da nake da wata alaƙa da shi ta kudi, sanayya, iyali (ko dangantaka mafi kusa ta kawance) ba
- Zan nemi izini kafin yarda a zaɓe ni a matsayin mai takara ko wani matsayin ofis daban na kowace jam'iyyar siyasa
- Ba zan karɓi kyaututtuka masu mahimmanci ko kowane biyan kuɗi daga gwamnatoci, al'umma da muke aiki da su, masu ba da kuɗin tallafi, masu kawo kaya da sauran mutane wadanda aka hada ni da su don aikina tare da [NGO] ba

**Rike sirri**

- Zan lura sosai a dukkan al'amuran harkar ofis, kuma ba zan bayyana kowane bayanin sirri game da abokan aikina ba, al'amuran da suka shafi aiki ko kowane bayanin sirri sai dai in shari'ah ta buƙaci hakan

# Korafe-korafe da kai rahotanni

Ya zama wajibi ga ma'aikatan [NGO] su jawo hankalin manajan da ya dace game da kowace matsala, cin zarafi ko damuwa da suka shaida, da aka sanar da su, ko suna zargin abin ya nuna cewa an sabawa Ka'idojin dake cikin wannan Dokar. Ma'aikatan [NGO] da suke bayar da rahoton damuwa an kare su ta Ka'idar Bayyana Rashin Da'a a Wajen aiki.

Ma'aikatan da suke da korafi ko damuwa game da sabawa Dokar ya kamata su bayar da rahotonsa nan take zuwa manajansu. Idan ma'aikacin yana tsoron bayar da rahoton zuwa manajansa (misali idan suna jin cewa ba za'a ɗauki rahoton da mahimmanci ba, ko in damuwar ta shafi mutumin) za su iya bayar da rahoton zuwa kowane ma'aikaci daban da ya dace. Misali, wannan zai iya zama babban manaja ko wani ma'aikacin ɓangaren HR.

Ma'aikatan da suke karɓar rahotanni ko damuwa ya zama dole su ɗauki mataki ko bayar da rahoton nan take bisa ga Ka'idoji da hanyoyin Korafe-korafe na [NGO]

# Ka'idoji masu alaƙa

Ka'idar Korafe-korafe da Hanyoyin kai su

Ka'idar Lafiya da Tsaro a Wajen aiki

Ka'idar Bayyana Rashin Da'a a Wajen aiki

Ka'idar Hana Magudi da Rashawa

Ka'idar Kiyayewa

Manufar Hana Tsangwama da Tursasawa

*Godiya ga CHS Alliance*

Manufar Tsaro

Manufar Amfani da IT

___

A karɓar aikina na yi alƙawarin yin ayyukana kuma in tsara halayena bisa ga buƙatun wannan Dokar

Suna:

Sa hannu:

Kwanan wata: